UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# KAYAN AIKI DON AIKI DA AL'UMMOMI DAGA NESA

**SHIN KA NA SO KAYI SADARWA DA AL'UMMOMI KUMA KA SHIGAR DASU DAGA NESA (MUSAMMAN A WANNAN YANAYIN COVID-19)? GA WASU DABI'U MASU KYAU DON AIKI TARE DA AL'UMMOMI WAJEN GANO BUKATUN SU DA NEMAN MASLAHA GA MATSALOLIN SU.**

## REDIYON AL'UMMA

### MEYASA?

- Rediyo yana taimakawa da isar da bayani mai matuƙar mahimmanci wanda zai iya ceton rayuka zuwa mutane da yawa.
- Kuma wata hanya ce don tattaunawa wanda yake bari mu samu bayani akan ayyukan UNHCR da abokanai aikinsu.
- Za'a iya sadarwar rediyo ta ƙananan tallace-tallace don bada takaitaccen bayani.
- Kuma za'a iya amfani da shirye-shiryen rediyo (awa 1 zuwa biyu 2) tare da sashin kira don samun bayanai sosai daga jama'a, da kuma tattara ra'ayoyi da damuwa daga al'ummomi.

### ANA BADA SHAWARAR SHI

- Yi wani bincike akan lokutan da bayanai da suka fi dacewa. Don bari kowa ya samu shiga (mata, maza, yara maza da yan mata), dole shirye-shiryen rediyo suyi la'akari da rawar da jinsi yake takawa kuma suyi shirin a lokutan da za'a samu rukunai jama'a daban-daban.
- Yi la'akari da matsalolin samun rediyo saboda ba kowane gida keda rediyo ba. Kodayake wasu "ƙananan" wayoyi nada abun kama FM, amma duk da haka ba kowa a cikin al'umma ke iya samun wannan.
- Bada zaɓin yin rikodin bayanin (podcast) da kuma turawa cikin aminci (ta Bluetooth, misali).

## LAYIN KIRA NA KAR TA KWANA

### MEYASA?

- Layin kira don taimako na taimakawa da sadarwa tare da al'umma.
- Yana da amfani sosai idan ba kuwa cika haɗuwa da mutanen da abun ya shafa, kamar biranen da jama'a sunyi yawa ko a wurare masu nesa

### ANA BADA SHAWARAR SHI

- Layin kira don taimako na iya zama da tsada don haɗawa. Neman ƙari daga ofisoshin UNHCR na ƙasar da abokanai aiki na UNHCR.
- Jawo hankali tsakanin al'ummomi akan layin kar ta kwana: menene ake yi dashi? menene iyakar shi?
- Horar da ma'aikata da/ko masu sa kai wanda zasu zama masu karɓar kira

UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

## SMS (SAKONNIN WAYA)

### MEYASA?

- SMS wani kayan aiki ne mai samuwa wanda yake sa a samu isar da bayani zuwa mutane da yawa a manyan yankuna. Ana iya tura sakonnin waya a harsuna daban-daban
- SMS yana bari ka samu bayani akan gamsuwar al'umma ko yi bincike
- Ana iya adana sakonnin akan wayar kuma wanda aka turawa sako na iya nunawa ko turawa wasu mutane
- SMS na amfani da sabis kaɗan, saboda haka ya dacewa yankunan inda sabis ɗin bai da ƙarfi sosai

### ANA BADA SHAWARAR SHI

- Za'a iya ware wasu rukunai jama'a (kamar matar da suka yi hijira daga wasu ƙasashe wanda basa samun damar waya, makafin da basa iya karatu...)
- Yi wani binciken bayanin da buƙatun sadarwa na al'ummomin, don sanin idan SMS na daga cikin hanyoyin da suke amfani dashi (ko kuma zasu so amfani)
- Amfani da SMS na buƙatar kasafin kuɗi da/ko yarjejeniya da kamfanin sadarwa na gida

## SHAFUKAN SADA ZUMUNTA

### MEYASA?

- Shafukan sada zumunta (Facebook, Twitter, Instagram, WhatsApp, da sauransu) na bada damar isar da bayani zuwa mutane da yawa da wuri fiye da sauran hanyoyin jawo hankalin jama'a na gargajiya.
- Shafukan sada zumunta wani kayan aiki ne mai kyau don sadarwa tare da al'ummomi (tattaunawar gungu, musayar bayanai...)
- Yana barin ka tura sakon rubutu, hotuna, sauti da bidiyo, taswira da takardu
- UNHCR na wallafa bayanai ƙasar na musamman akan shafin yanar gizo Help.UNHCR.org

### ANA BADA SHAWARAR SHI

- Gina aminci: bada bayani daidai wanda za'a fahimta da sauki don ƙarfafa aiki tare da al'ummomin da abun ya shafa
- Nema ƙarin bayani game da kare bayanai mutane sa sirri. Kada ku wallafa bayanai wanda zai sa a gano mutanen
- Yi la'akari da wasu rukunai jama'a da basa cika samun damar intanet da fasaha (kamar mata, tsofaffi da yara). Karfafa da wasu kayan aiki na mu'amala da al'umma



Akwai ƙarin kayan aiki da shawarwari don sadarwa tare da al'ummomi akan shafin yanar gizo: cwc.westafrica.exposed